# Haramta duk wani horo mai tsanani ga yara

## Amsoshi ga tambayoyin da aka fi yi



Amsoshi ga tambayoyin da aka fi yi:

**Haramta duk wani horo mai tsanani ga yara:**
Tambayoyi da amsoshi don yara da matasa

**Haramta duk wani horo mai tsanani a makarantu:**
Amsoshi ga tambayoyin da aka fi yi

AN BUGA A 2009 NA:

**Gamayyar Kasashe don kawo Karshen Horo mai Tsanani ga Yara**

AN BUGA 2017 NA:

**Gamayyar Kasashe don kawo Karshen Horo mai Tsanani ga Yara**

www.endcorporalpunishment.org

Gamayyar Kasashen duniya don kawo Karshen Horo mai Tsanani ga Yara.
Anyi rijista a Ingila da Wales a matsayin kamfani mai lamba 2354395 da
lambar cibiyar tallafi: 328132.

Ofishi: The Foundry, 17 Oval Way, Landan SE11 5RR, UK.

**Save the Children Sweden**

www.raddabarnen.se; resourcecentre.savethechildren.net

Save the Children ta Sweden wata bangare ce ta kungiyar Save the
Children, cibiya da ta kunshi kungiyoyin Save the Children 29, da aka yi
wa rijista a Swizalan kuma daya daga cikin kungiyoyin kare hakkin yara da
suka fi girma a duniya. Kungiyar Save the Children bangare ne na Save the
Children International (SCI), wadda ita ce ke aiwatar da ayyukan kungiya.

Babban Ofishin Save the Children ta Sweden: Rädda Barnen,
SE-107 88 Stockholm, Landsvägen 39, Sundbyberg, Sweden.

Aduk lokacin da muka yi tunanin haramta duk wani horo mai tsanani ga yara tambayoyi da yawa na tasowa, musamman idan an dangantasu da me haramcin zai haifar ga iyaye da rayuwar iyali. Wannan dan littafi zai bada amsoshi ga tambayoyin da aka fi yawan yi, ya kuma warware abubuwan da ba a fahimta ba a kan dalilan haramcin da kuma tasirinsa ga iyalai.



# Tambayoyi

**Sashi na 1: Tambayoyi akan dalilan haramta duk wani horo mai tsanani**

**8** Shin horo mai tsanani na cutarwa?

**10** Me yarjejeniyar kasa-da-kasa ta majalisar dinkin duniya ta zartar akan Hakkokin Yara, kuma me tace akan horo mai tsanani ga yara?

**12** Rayoyin jama'a sun nuna cewa, yawancin mutane ba sa goyon bayan yin dokar haramta horo mai tsanani ga yara. Shin ba za mu saurari masu wannan ra'ayi ba?

**13** Na kan ji matasa na maganar goyon bayan horo mai tsanani. Anya ma iya saurarensu kuwa?

**14** Dukan da aka yi min ina yarinta bai cutar da ni ba ko kadan. Anya zan sami kaina a inda nake yanzu inda mahaifana ba su ladabtar da ni da duka ba?

**17** Akwai keta hakkokin yara masu muni da yawa – me ya sa aka fi mai da hankali ga wannan?

**18** Iyaye na da hakkin horon yaransu yadda suka ga dama. Ba kamata yayi a kalubalance su kadai ba a wuraren da suka wuce iyaka har suka kai ga cin zarafin yaran?

**20** Akwai banbanci mai yawa tsakanin dukan yaro da talle keya. Haramta horo mai tsanani bai wuce iyaka ba kuwa?

**23** Me zai hana a fassara duka mara cutarwa, a maimakon haramta shi gaba daya?

**24** Addinina ya bani damar amfani da horo mai tsanani. Anya ba tauye hakki ba ne hana ni amfani da shi?

**26** Me zai sa a kawo doka a cikin wannan batu? Me zai hana a ilmantar da iyaye su guji amfani da horo mai tsanani?

27 Yawancin horo mai tsanani na faruwa cikin gidan iyalai, a kebantaccen wuri; zai yi wuya a haramta shi. To menene dalilin haramta shi bisa doka?

28 Shin ba za mu jira har sai yanayi ya sauya ga iyaye da malamai ba kafin a haramta horo mai tsanani, don kar hakan ya kara musu damuwa dangane da tarbiyyar yara?

31 Haramta horo mai tsanani tsari ne, na turawa. Horo mai tsanani yana cikin tsarin tarbiyyar yara a al'adata. Ba shishshigi ba ne ba haramta shi?

32 Me ya sa daina dukan yara ke da wahala?

**Sashi na 2: Tambayoyi akan tasirin haramta duk wani horo mai tsanani ga yara**

36 In aka tilastawa iyaye daina horo mai tsanani, hakan ba zai sa lalacewar yara ba su zama ba tarbiyya?

39 In aka haramta horo mai tsanani, wannan ba zai sa a muzgunawa yaran ba ta hanyoyin da za sufi yin barazana ga tunaninsu?

40 In aka sa horo mai tsanani cikin manyan laifuka, ba za a daure iyaye da yawa ba kuma hakan yasa a karbe yara da yawa a kai su gidajen reno?

42 Shin ba daidai ba ne iyaye su dan doki yara kadan dan hanasu cutar da kansu?

# Sashi na 1: Tambayoyi akan dalilan haramta duk wani horo mai tsanani



# Shin horo mai tsanani yana cutarwa?

Eh, yana cutarwa! Yana cutarwa a jiki da kuma kwakwalwa. Cikin binciken da aka yi a duk duniya, yara sun fadi yadda horo mai tsanani ke cutar da su. Binciken Sakatare Janar na Majalisar Dinkin Duniya kan Cin Zarfin Yara, wanda aka kammala a 2006, shi ne cikakken bincike na farko a duniya kan yanayi da girman matsalar. Kwararren da ya jagoranci binciken, Professor Paulo Sérgio Pinheiro, ya rubuta a rahoton cewa:[1]

“A dukkan binciken da aka gudanar, yara sun yi matukar nuna bukatar a haramta duk wannan cin zarafi na horo mai tsanani. Yara sun nuna cewa suna cutuwa ta kowacce fuska – a zahiri, har a badini – sakamakon horo mai tsanani. Amincewar iyaye da amfani da horo mai tsanani wajen tarbiyya shi ma yana sa yara cikin mawuyacin hali sosai na cutuwa.

“Ya kamata gwamnatoci su dauki wannan a matsayin batun da yake bukatar matakan gaggawa na nan take, duk da cewa matsalar horo mai tsanani ba wani sabon abu ba ne. Tsawon shekaru aru-aru yara suna fuskantar cin zarafi daga na gaba dasu. Amma yanzu yadda illar horo mai tsanani ta bayyana a fili, bai kamata a bar lamarin ya ci gaba ba. Yara suna bukatar kariya da ta kasance hakkinsu akan al’umma.”

1. Pinheiro, P. S. (2006), Bayanin Duniya a kan Cutar da Yara, Geneva: Seckatari-Janar Majalisa Dinkin Duniya UN Karatu a kan Rikici Game da Yara. Don karin bayani kan Nazarin da kuma saukar da rahoto duba www.ohchr.org/EN/HRBodies/CRC/Study/Pages/StudyViolenceChildren.aspx.

Haddasa ciwo a jikin yaro shi ma take 'yancin yara ne na kariya ne daga cin zarafi – kuma manya ba sa la'akari da banbancin girma da karfi da ya banbanta su da yaran, da kuma tasirin da wannan banbancin zai jawo sakamakon zafin raunin da yaron zai ji. An fadada bincike, inda aka tambayi iyayen yara kan irin zafin "duka" da suke ake amfani da shi ga yaransu. An gano cewar biyu daga cikin biyar sun yi amfani da karfin duka fiye da yadda aka nufa.[2] Kuma binciken Kwalejin Ilimin Tabuwar Kwakwalwa ta Landan ya tabbatar da tasiri ga aikin kwakwalwa yayin da aka yi amfani da karfi a yanayin doki-in-doka. Hakan na haddasa karuwar amfani da karfi da rashin tantance yawa ko girman hukuncin da ya dace a yi amfani da shi wajen horon yara.[3]

Bugu-da-kari, manya ba sa damuwa da cutarwa ta kwakwalwa da horo mai tsanani ke jawowa, tasirinsa ga kimar yaron da kuma illar da ya ke haddasawa, yanzu ko kuma nan gaba a rayuwa, da kuma tasirin da zai shafi al'umma baki daya. Gamayyar Kasashen Duniya na sane da fiye da bincike 250 kan tasirin horo mai tsanani da yake da alaka da illoli barkatai ga lafiya; da kuma illa ga lafiyar kakwalwa, dusashewar fikira, cin maki kadan a makaranta, saurin fushi, wahalar bayyana nagarta da rashin mu'amala mai kyau da mutane. Wannan zai yi tasiri har zuwa girmansu.[4]

2. Kirwaun, S. & Bassett, C. (2008), Presentation to NSPCC: Physical punishment, British Market Research Bureau/National Society for the Prevention of Cruelty to Children.

3. Shergill, S. S. et al (2003), "Two eyes for an eye: The neuroscience of force escalation", Science, vol. 301, 11 July 2003, p. 187.

4. Don karin bayani, duba azabtar da yara: takaitaccen bincike kan tasirinsa da kungiyoyi, a endcorporalpunishment.org/resources/research.

# Me yarjejeniyar kasa-da-kasa ta majalisar dinkin duniya ta zartar akan Hakkokin Yara, kuma me tace akan horo mai tsanani ga yara?

Yarjejeniyar kasa-da-kasa ta Majalisar Dinkin Duniya (MDD) kan Hakkokin Yara, ko UNCRC, a tarihi ita ce cikakken bayani na hakkokin yara da aka taba samarwa, kuma ita ce wadda mafi rinjayen kasashe suka amince da ita a matsayin yarjejeniyar kasa-da-kasa. Yarjejeniyar na da dokoki 54 da suka hade duk rayuwar yaro, kuma ta gindaya hakkokin dukkan wani yaro; ta fuskar zamantakewa, tattalin arziki, al'adu da kuma siyasa.

Kwamitin MDD na hakkokin yara aka dorawa nauyin tabbatar da kasashen da suka sun aiwatar da wannan yarjejeniyar kasa-da-kasa sau-da-kafa da kuma tabbatar da ita. Kwamitin ya nuna a fili cewar UNCRC na bukatar haramtawar bisa doka, kuma a hana aiwatar da duk wani horo mai tsanani a ko ina – a gida, wuraren raino, makarantu da wuraren horarwa.

Bayanin Gama-gari na Kwamitin No. 8 (2006) kan “Hakkin yaro na kariya daga horo mai tsanani da wasu nau'ukan horon keta da (kaskanci, sakin layi 19;28. 2; da 37, da wasu)” an tabbatar da wadannan wajibci, wanda aka jaddada a Bayanin Gama-gari No. 13 (2011) kan “Hakkin yaro na 'yantuwa da kariya daga dukkan cin zarafi”.

Kwamitin na lura da kasashen da suka aiwatar da yarjejeniyar UNCRC akai-akai kuma a karshen aikin sa ido da suka yi sun bada shawarar haramta horo mai tsanani. Wasu bangarorin masu sa ido bisa yarjejeniyar suna kara bada shawarar haramta horo mai tsanani ga yara kuma ana kara tada wannan batu a tarukan shekara-shekara dake Nazari akan hakkin bil'adama a dukkan kasashen duniya.

# Ra'ayoyin jama'a sun ce yawancin mutane ba sa goyon bayan haramta horo mai tsanani a dokance. Shin ba za mu saurari masu irin wannan ra'ayi ba

Dangane da wannan batun – kamar sauran; hada da cin zarafin mata da wariyar launin fata – ya dace 'yan siyasa su yi jagoranci, ba su bi ra'ayin jama'a ba. Abinda ya kamata a baiwa muhimmanci shi ne; dole gwamnatoci su tabbatar da dokoki da zasu kare yara da kuma basu kariya ga mutuncinsu, kamar manya.

Kusan duk kasashen da suka haramta horo mai tsanani ga yara, sun yi hakan kafin jin ra'ayin jama'a, sai kuma nan da nan, daga baya ra'ayin jama'ar ya goyi bayan canjin. Cikin shekaru kadan za mu yi mamaki – kuma zamu ji kunya – idan muka yi waiwaye muka duba zamanin da da aka amince da yin amfani da horo mai tsanani akan yara.

Sakamakon jin ra'ayin jama'a akan wannan batu, ya danganta da yadda aka tsara tambayoyi da kuma yawan bayanan da masu ba da amsar ke da su. In mutane suka sami cikakken bayani akan abin da ke faruwa yanzu na rashin kariya ga yara da kuma dalilin haramta horo mai tsanani, za su goyi bayan haramcin – kuri'un jin ra'ayi jama'a sun nuna sakamako mabanbanta in aka yi tambayoyi akan wannan batu ta hanyoyi daban-daban.

# Na kan ji matasa na maganar goyon bayan horo mai tsanani. Ma iya sauraronsu kuwa?

Gaskiya ne wani lokaci yara za su ce yana da kyau a dake su, wai yana koya musu yadda zasu zama masu halin kirki, ko kuma ma duka na nuna mahaifansu na son su. Dole mu saurari abun da matasa suke fada. Amma manya suna da alhakin su fahimci abun da yara suke fada mana ba kawai ji ba. Dama mun riga mun jawo hankali akan abubuwan da yara suka fara fada mana game da bacin ran su a fili da a zuciyar su wanda horo mai tsanani ko azabtarwa suka jawo (duba 'Azabtarwa ta na da zafi kuwa', a shafi 8). Idan wasu yara sun ce kamar dole a yi musu horo mai tsanani kuma yana da kyau, sun nuna irin yadda suka girma da imanin cewa daidai ne a azabtar da mutum kuma sun dauka shi ne daidai kuma sun yi imani da shi, sun rike ra'ayi da halayyar iyayensu.

Yara suna da cikakken hakkin a kare martabarsu da kuma kare 'yan cinsu a matsayin bil adama da kuma darajanta jikinsu, kuma da kariya daga cutarwa. Hakki ne akan gwamnati su tabbatar cewa doka ta kare wadannan 'yancin. Alhaki ne akan iyaye da sauran magabata su tabbatar yara sun san 'yan cinsu.

# An min duka ina yaranta kuma bai cutar da ni ba ko kadan. Anya zan sami kaina a inda nake yanzu in da mahaifana ba su ladabtar da ni da duka ba?

Babu wanda ya san yadda zai zama inda iyayen mu basu taba mana duka ko wulakanta mu ba. Kuma mutane da yawa sun ce, duka bai cutar da su ba suna boye irin kuncin da suka fuskanta a lokacin da manya mafi kusa dasu suka yanke hukuncin cewa hanya kadai da zasu yi amfani da ita wajen horo ita ce, azabtarwa.

Manya da suke dukan 'ya 'yansu da sunan ladabtarwa yawanci suna yi ne saboda su kansu an musu duka a lokacin yaranta. Duk da cewa bincike ya nuna galibi suna jin laifi a ransu bayan sun yiwa yara duka, suna ci gaba da bugun yaran, musamman in hakurinsu ya kare. Ba daidai ba ne a dora alhakin wannan lamari akan magabata, saboda suna aiki ne da muguwar al'ada da suka tarar ana amfani da ita. Amma ba daidai ba ne mu ki canji saboda muna tsoron a ce mun yi wa iyaye da magabata tawaye. Lokaci yana canzawa, kuma zamani yana ci gaba. An amince cewa yara suna da hakki na bukatar daukar mataki na kawo karshen dokoki da al'adu da suka amince da yin amfani da horo mai tsanani wajen tarbiyya, kamar yadda aka tashi tsaye wajen kawo karshen amincewa da cin zarafin mata.

Wasu mutane na cewa: "An doke ni a lokacin yarinta kuma na zama mutum nagari." Amma akwai mutane da suka fuskanci munanan abubuwa iri-iri a lokacin da suke yara kuma sun zama "mutanen kirki" da suka girma, amma ba wanda zai ce munanan abubuwan da suka fuskanta a lokacin yarinta suna da kyau. Galibi yadda suka fuskanci munanan abubuwan da aka yi musu suna yara shi ne yake taimakonsu, amma ba wai ainihin azabtarwar da suka fuskanta ba.

"Amma babu kyau **ka ki canji** saboda tsoron nuna kamar muna sukar abubuwan da iyayen mu suka yi."

"Amfani da azabtarwa wajen **horo** shi ne nau'in cin zarafin yara mafi yawa."

# Akwai keta hakkokin yara masu muni da yawa - me ya sa aka fi mai da hankali ga wannan?

Kamar yadda hukumar UNICEF ta bayyana, amfani da azabtarwa wajen yin tarbiyya shi ne sannnen hanyar cin zarafin yara da matasa.[5] Horo ta hanyar azabtarwa yana haddasa kisan dubban yara da kuma haddasa munanan rauni ga miliyoyin yara a duniya kowacce shekara. Wannan babbar matsala ce.

Wannan ba matsalar kare yara daga cin zarafi ba ce kawai. Amincewar shari'a dangane da amfani da azabtarwa wajen horon yara a kasashe da dama alama ce ta irin kaskancin da yara suke fuskanta, inda ake daukar su a matsayin mallakar iyaye maimakon a dauke su a matsayin mutane masu hakkoki. Yara da yawa a duk kasashen duniya suna fuskantar amfani da azabtarwa wajen horo kowacce rana, kuma ta haka ne ake keta hakkin yara. Kamar yadda haramtawa da kuma yaki da cin zarafin mata ya zama babban abun daya karfafa mata da kuma amincewa da hakkin su, haka ya kamata ya kasance ga yara. Haramta azabtar da yara da sunan horo zai kare kimar su kuma ya canza yadda al'umma take kula da su. Babu wata kasa da zata bugi kirjin cewa, tana kare rayuwar yara da manya, ko ikirarin amfani da tsarin kare yara, alhali kuwa ana amfani da azabtarwa wajen horon yara.

5. UNICEF (2014), Hidden in Plain Sight: A statistical analysis of violence against children, NY: UNICEF

# Iyaye na da hakkin tarbiyyantar da yaransu yadda suka ga dama. Shin ba kamata yayi a kalubalance su indai sun wuce gona da iri ba ta hanyar amfani da cin zarafin yara?

Zamani na canzawa; daga daukar yara tamkar mallakar iyaye zuwa ganin su a matsayin mutane masu hakki. Yara su ma bil adama ne, suna iya cin moriyar hakkokin dan adam – kuma wannan bai tsaya a bakin kofar gidan su ba. Yara suna da hakkokin kariya daga duka kamar sauran mutanen gidansu, kuma yanzu ba shishshigi ba ne a rayuwar iyalai ana cewa doka ta kare yara daga zalunci a cikin gida fiye da batun kare manya daga cin zarafi cikin rayuwar aure.

Yarjejeniyar majalisar ɗinkin duniya akan haƙƙoƙin yara ta bada karfi sosai ga muhimmancin iyalai da kuma nauyin da ya rataya akan iyaye, inda aka fi bada muhimmanci ga kula da yara da kuma tarbiyyarsu (bayani 18). Wasu mutane suna da ra'ayin cewa, amfani da azabtarwa da sunan yin tarbiyya a karshe zai amfani rayuwar yara nan gaba. Amma kamar yadda kwamitin kare hakkin yara ya nuna:[6]

"...baiwa bukatun yara muhimmanci fassarar ya zama, har da hakkin kare yara daga duk wani nau'in cin zarafi da kuma bukatar bada mahimmanci ga ra'ayoyin yara; ba wata hujja da za'a yi amfani da ita wajen kare mummunar al'ada, kamar amfani da azabtarwa wajen horo ko kuma dukkan wani horo na kaskanci da wulankanci ko mugunta, wanda yake tasiri akan darajar yaro da kuma hakkin kare jikin shi."

A karshe, iyaye zasu amfana daga sakon dake nuna cewa, horo ta hanyar azabtarwa yana kawo illa ga zamantakewar iyali da kuma wasu illolin da dama da zasu shafi yara, kuma su yi musu mummunan tasiri.

6. Bayanin Janar No. 8 (2006) on "Hakkin yaro na kariya daga horo mai tsanani da wasu nau'ukan horon keta (da kaskanci. sakin layi 19;28. 2; and 37, inter alia)", sakin layi 26, akoi a endcorporalpunishment.org/wp-content/uploads/key-docs/CRC-general-comment-8.pdf.

# Akwai banbanci mai yawa tsakanin dukan yaro da mari kadan maras zafi. Shin haramta dukkan horo na azabtarwa bai wuce gona da iri ba kuwa?

Dukan yaro daban yake da "mari kadan" (amma duba 'Shin Azabtarwa tana illa kuwa', a shafi 8), amma duk tafiyarsu daya, dukkansu cin zarafi ne kuma sun keta hakkin yara na a kare martabarsu da kuma kare jikinsu daga kowacce irin azaba. Al'umma baza su bada hujja ba ko kuma su yi kokarin goyon bayan kowanne matakin azaba ba idan suna yaki da cin zarafin tsoffafi. To me yasa za su bada hujjoji na kare azabtar da yara? Kuma ya kamata a gane hadarin yin amfani da azaba wajen nuna so ga yara. Dukan yara da sunan nuna musu kauna bai dace ba. Ana amfani da kalmar kauna wajen boye illar amfani da azabarwa wajen horon yara.

Wasu mutane suna cewa "akwai banbanci mai yawa tsakanin cin zarafin yaro da mari kadan," ba tare da maida hankali ga girman azabar dake cikin duka komai kankantarsa ba. Ba gaskiya ba ne a ce wai manya suna iya kiyasta yawan dukan da suke yi wa yara. Bincike ya nuna cewa galibi ana amfani da karfi fiye da yadda aka yi niyya,[7] kuma azabar tana karuwa.[8] Sannan kuma, ko yaya tsananin dukan yake, ya keta hakkin yaro da kuma darajar jikin shi.

7. Kirwaun, S. & Bassett, C. (2008), Presentation to NSPCC: Physical punishment, British Market Research Bureau/National Society for the Prevention of Cruelty to Children.

8. Shergill, S. S. et al (2003), "Two eyes for an eye: The neuroscience of force escalation", Science, vol. 301, 11 July 2003, p. 187.

Masu yin dokoki da gwamnatoci suna banbanta "cin zarafin yara" da "azabtarwa", amma yawancin cin zarafi azabtarwa ne – manya suna cin zarafin yara don azabtar da su, da kuma samun cikakken iko akansu. Ba a kallon lamarin ta wannan fuska idan aka zo ga batun cin zarafin tsofaffi, inda ake nuna rashin amincewa da kowacce irin azaba mai yawa ko kuma kadan. Amma dangane da batun yara manya sun bullo da wani tsari na banbanta duka domin horo (wanda an amince da shi) da kuma azabtarwa (da ba a amince da ita ba) Amma a zahiri, ba wani banbanci tsakanin horo mai tsanani da azabtarwa.





"Babu wani abu wai mari mara cutarwa."

# Me yasa ba za'a bada ma'anar mari mara cutarwa ba, maimakon haramta shi gaba daya?

Babu wani irin mari ko duka da baya cutarwa. Duk duka ko mari na keta darajar jikin yara kuma ya nuna rashin girmama mutuncin dan adam. Bincike da yawa sun nuna azabtarwa mara tsanani daga iyaye kan zama hadari da zai kai ga mummunar azabtarwa da zata iya zama cin zarafi, kuma akwai yiyuwar duka zai iya karuwa, kuma an riga an fada cewa; ba za a iya tantance yawan karfi da aka yi amfani da shi ba wajen horo (duba 'akwai banbanci tsakanin dukan yaro da mari mara cutarwa. Shin haramta azabtarwa bai wuce gona da iri ba?' shafi 20).

Wasu kasashe sun yi kokarin kayyade hanyoyin dukan yara – a wanne shekaru ne za a yi dukan, a wanne bangaren jiki, kuma da menene za a iya yin dukan, da dai sauransu. Baya ga aika sako mai rudarwa ga iyaye dangane da azabtar da yara, irin wadannan ka'idoji basu da wani amfani kwata-kwata. Ba zamu yi tunanin bada amintattun hanyoyin cin zarafin mata, ko tsoffafi, ko wasu gungun jama'a ba. Dan haka yara suna da cikakken hakkin samun kariya daga azabtarwa ko cin zarafi. Dole a yi la'akari da cewa, yara kanana ne kuma jikinsu ba shi da kwari ko girma – jikinsu yana da rauni kuma sun fi kowa kasancewa cikin hadarin samun rauni – suna da hakkin mu tabbatar mun kare su daga kowacce irin azabtarwa ko cin zarafi.

# Addini na ya bani damar amfani da horo mai tsanani. Ba nuna banbanci ba ne idan an hana ni amfani da horo mai tsanani?

Dukan yaro ya sabawa manufofin dukkan manyan addinan duniya, wadanda suka bada muhimmanci ga tausayi, yin adalci da kuma kare masu rauni. Mabiya manyan addinan duniya suna kwaikwayon rayuwar wadanda suka kawo sakon addinan ga duniya. Masana da kuma manyan malaman addinai dukka sun bayyana cewa babu wata shaidar cewa wadanda suka kawo sakon addinan ga duniya sun taba duka ko azabtar da yara.

Ra'ayin addini wanda ya goyi bayan horo mai tsanani ga yara galibi yana da alaka da dabi'u na al'ada da kuma kokarin nuna karfi da iko da yara. Irin wadannan al'adu sun dauka cewar biyayya ido rufe ita ce tarbiyya, kuma sun dauka yin amfani da azbatarwa wajen horo shi ne hanyar gyara halayen yara da koya musu "ladabi".

Malaman addini na hadin gwiwar kasashen duniya domin kawo karshen yin amfani da azabtarwa wajen horon yara suna kokarin kawo karshen horo mai tsanani ga yara. Fiye da malaman addini dari takwas (800) da suka halarci taron duniya na addinai domin wanzar da zaman lafiya a birnin Kyoto, a kasar Japan (2006) sun goyi bayan kudirin Kyato na tabbatar da addinai sun yi kokarin kawo karshen cin zarafin yara (Kyoto Declaration)[9] – wanda yake rokon gwamnatoci su kafa dokoki da zasu haramta kowanne irin cin zarafi ko horo mai tsanani ga yara.

9. Ana samun cikakken bayanin wannan sanarwar a churchesfornon-violence.org/wp/wp-content/uploads/2012/02/Violence-Against-Children-3.pdf.

Kwamitin Hakkokin Yara, a cikin bayanin sa lamba takwas (8), ya amince cewa za a iya baiwa hakkin dan adam muhimmanci fiye da komai.[10] Kwamitin ya ce:[11]

"Akwai hujjoji da wasu addinai ke bayarwa akan horon yara mai tsanani, da kuma fassara cewa addini ya amince a yi horo mai tsanani kuma yin hakan wajibi ne. Amma akwai dokokin 'yancin addini na duniya da suka baiwa kowa damar a kare mutuncinsa da kuma darajarsa, bisa yajejeniya akan Hakkokin Jama'a da Siyasa na kasa-da-kasa (bayani na goma sha takwas 18) dole dukkan addinai su kiyaye da kuma kare hakki da darajar dan adam."



10. Bayani kai tsaye, No. 8 Sakin layi. 29.
11. Bayani kai tsaye, No. 8 Sakin layi. 29.

# Me zai sa a kawo doka a cikin wannan batu? Me zai hana kawai a ilmantar da iyaye su guji amfani da horo mai tsanani?

Kawo karshen duk horo mai tsanani da wasu nau'ukan horo na keta ko kasknaci na bukatar ilimantarwa da kuma haramtawa bisa doka. Wannan shi ne kadai zabin da ake da shi. Hakkokin bil adama sun bukaci cewa a baiwa yara kariyar doka daidai da manya – a cikin gida da ko ina. Kuma a soma hakan yanzu. Doka ita ma tana da muhimmanci wajen ilimantar da iyaye. Kuma yana da muhimmanci kowacce doka a hada ta da ilimantarwa. Haramtawa za tasa iyaye su nemo sabbi kuma kyawawan hanyoyin yiwa yara tarbiyya, kuma hakan zai karfafa masana, ‘yan siyasa da kuma kafofin yada labaru wayar da kan jama’a.

Yana da wuya da kuma rikitarwa a wayar da kan iyaye su daina abinda doka ta amince da shi. Abinda mutane suke cewa shi ne; idan har abu doka ta amince da shi to ba shi da matsala. Dan haka ilimantarwa zata yi amfani ne kawai idan doka ta amince da abinda ake ilimantarwa akai.

# Yawancin horo mai tsanani na faruwa ne a cikin gida, cikin iyali a kebantaccen wuri; zai yi wuya a haramta shi. To menene dalilin haramtawar?

A yanzu babu wanda zai ce kada a haramta cin zarafi tsakanin ma'aurata saboda kawai yana da wahala a aiwatar da haramcin; dan haka me yasa ba za'a kare yara daga horo mai tsanani ba? Farkon dalilin gyara dokar haramta horo mai tsanani shi ne hanawa – don hana mummunan horo akan yara kafin ya faru. Hana aukuwar abu shi ne farkon amfanin kowacce doka mai tasiri: don kafa ka'ida da kuma aika sako, sakon da zai shiga har cikin gida, cikin "sirrin" gidan iyalai. Amma haramta horo mai tsanani abu ne da za'a yi shi cikin matakai, domin kare yara – duba 'idan horo mai tsanani ya zama laifi, shin ba za a hukunta iyaye dubbai ba, kuma a karshe sai an kai yaran gidajen riko ko reno?' shafi na 40.

Kuma soma aiwatar da haramtawa zai fara ne tare da wayar da kan iyaye ta yadda zasu fahimci tsarin tarbiyya ba tare da horo mai tsanani ba.

# Shin baza mu tsaya har sai yanayi ya sauya ga iyaye da malamai ba kafin a haramta horo mai tsanani, don kar hakan ya kara musu nauyi da damuwa?

Wannan batu ya nuna amincewa da gaskiyar cewa, horo mai tsanani yawanci kawai wata hanya ce da iyaye suke amfani da ita wajen huce wata damuwa dake cikin ransu, amma ba wai hanya ce ta bada tarbiyya ba. A gidaje da yawa da makarantu manya da iyaye suna bukatar kayan aiki da kuma tallafi, amma duk da matsalolin manya da iyaye suna da yawa basu da hujjar huce haushin matsalolinsu na rayuwa akan yara. Ba sai an jira matsalolin manya da iyaye sun ragu ba kafin a kare yara, kamar yadda ba a jira maza sun gyara halayensu ba kafin a kare mata daga cin zarafi.

Ta kowacce fuska aka duba dukan yara baya ragewa iyaye wata damuawa. Manyan da suke dukan yara idan suna cikin fushi daga baya suna jin kamar sun aikata ba daidai ba; wadanda suke dukan yara sosai suna maida yaran masu zama cikin fushi da bakin ciki a koda yaushe. Rayuwa a gidaje da wuraren bada horo inda aka daina amfani da horo mai tsanani domin ladabtarwa ta fi sauki sosai ga yaran da masu kula da su.

A kasashe da suke fama da rikici, manya da suke aiki da yara, har da iyaye da malaman makaranta, su kansu an taba azabtar da su kuma sun taba fuskantar wulakanci. Sun yarda a kare hakkokin yaran, amma tambayar ita ce wa zai kare nasu hakkokin? A zahiri, dole ne a magance matsalar keta hakokkin kowa, amma bai kamata a ce yara su jira har sai an kare hakkokin manya kafin a kare nasu hakkokin ba. Dukkan mutane suna da hakkin a kare hakkinsu da darajarsu kuma doka ta kare su – yara ma mutane ne kuma sun cancanci irin wannan kariya.



“Yara a fadin duniya **suna da hakkin** yin rayuwa ba tare da kowanne irin cin zarafi ba.”

# Wannan al'adar Turawa ce, da ta shafi wadanda suke kasashen Turai. Yiwa yara horo mai tsanani wani bangare ne na renon yara na al'adarmu. Anya ba nuna banbanci ba ne idan an haramta shi?

Tunanin cewa dukan yara wani abun alfahari ne na al'ada bai dace ba. Duk da haka dukan yara al'adar Turawa ce da suka yada a duniya ta hanyar cinikin bayi, mulkin mallaka da kuma koyarwar malaman mishan. Alal misali, a duk duniya ana amfani da kalamin Turawa dake cewa wai "horo mai tsanani daidai misali ya dace" wajen yin dokoki. Za'a iya cewa a al'adun da basu taba ko ba su cika dukan yara ba kadan ne kawai, kuma ana samun hakan ne tsakanin mutane masu rayuwa ta hanyar yin farauta, cikin daji, sune suke da al'adu da basu gurbata ba. Duk da cewa irinsu basu da yawa a yanzu saboda tasirin ci gaba da yadda duniya ta zama tsintsiya madaurinki daya.

Amma hakkokin bil adam ruwan dare ne gama duniya, kuma yara a fadin duniya na da hakkin rayuwa ba tare da kowanne irin cin zarafi ba. Duk al'adu na da alhakin kawo karshen horo mai tsanani, kamar yadda suka yi watsi da wasu al'adu da dama da suke keta hakkin bil'adama. Yarjejeniya majalisar dinkin duniya akan hakkokin yara ta amince a kare dukkan hakkokin yara da basu kariya daga kowacce irin cutarwa, ba tare da nuna banbancin launin fata, al'ada ko addini ba. Akwai kungiyoyi da suke fafitikar kawo karshen amfani da horo mai tsanani ga yara a kasashe da dama, a kowacce nahiya. A kasashe da dama a duniya an haramta dukan yara a makaranta ko wajen yin hukunci.

# Me ya sa daina dukan yara ke da wahala?

Idan manya da 'yan siyasa sun gano hanyar kawo karshen matsalar horo mai tsanani ga yara da tun da jimawa mun amince cewa yara suna da hakkoki kamar manya kuma ya kamata a kiyaye hakkokin yara domin kare darajarsu da kuma basu kariya bisa doka kamar kowa. Tabbas da mun soma la'akari da cewa yaran da suka soma rayuwa da rauni ko wasu matsalolin sune suka fi bukatar kariya fiye da manya.

Akwai dalilai da yawa da suka sa manya suka kasa daina yin amfani da horo mai tsanani wajen tarbiyya, saboda suna ganin hakkinsu ne su samu cikakken iko da yara:

(i) Abinda kowa ya sani. Mafi yawan mutane iyayensu sun musu duka a lokacin da suke yara. Yawancin iyaye sun yiwa 'ya yansu duka. Babu wanda yake tunanin iyayensa sun aikata ba daidai ba, ko basu masa tarbiyya mai kyau ba saboda duka. Wannan babban kalubale ne ga mutane da dama, da ma 'yan siyasa da masu fada a ji da kuma masu aiki a bangaren kare yara daga cin zarafi. Dukka wadannan zai yi wahala su kalli batun horo mai tsanani a matsayin batu da ya shafi daidaito da kuma kare hakki. Wannan ba batun dorawa wani ko wasu laifi ba ne. Su iyaye suna horo mai tsanani ne saboda haka aka saba yi. Amma lokaci yayi da za'a kawo karshen yi wa yara horo mai tsanani da sunan tarbiyya; a gina dangantaka mai nagarta tsakanin yara da iyaye.



(ii) Manya galibi na dukan yara ne saboda sun fusata, ko suna cikin gajiya, ko hakurinsu ya kare. Manya da yawa sun sani, har a cikin zuciyarsu, cewa suna dukan yara ne saboda huce haushi ko damuwar dake cikin ransu amma ba wai dan dukan zai taimaka wajen gyaran tarbiyya ba. Idan har aka ci gaba da yin haka duka zai zama hanya kadai da iyaye suke amfani da ita wajen gyara tarbiyya. Yana da wahala a canza halaye da aka jima ana amfani dasu, amma za'a iya canzawa. Yayin da gwamnatoci suka ci gaba da kashe kudade a fannin ilimi da kuma hanyoyi masu ma'ana na horon yara ba tare da amfani da duka ba iyaye zasu gano sabbin hanyoyi da dabaru na horo da tarbiyyar yara ba tare da amfani da duka ko horo mai tsanani ba. Ya kamata a samo hanyar kare mutuncin yara. Su kuma iyaye zasu gano hanyoyin horon hara ba tare da duka ba.

(iii) Rashin ilimi akan hanyoyi daban-daban. Dole ne a hada gyaran dokoki da kuma ilimantar da iyaye da yara da kuma al'umma baki daya akan hanyoyi masu nagarta da babu horo mai tsanani wajen yin tarbiyyar yara.



# Sashi na 2: Tambayoyi akan tasirin haramta duk wani horo mai tsanani ga yara



# Idan aka tilastawa iyaye daina yin horo mai tsanani, hakan ba zai kawo lalacewar yara, su zama ba tarbiyya?

A'a! Azabtarwa ba daya take da tarbiyya ba. Tarbiyya ta ainihi ba ta da alaka da amfani da karfi. Tarbiyya tana samuwa ne daga fahimtar juna, girmama juna, hakuri, fahimta, da sadarwa akai-akai a tsakanin iyaye da yara. Jarirai suna fara rayuwa bisa dogaro da iyaye da suke tallafa musu kuma su musu jagora a kowanne mataki har girmansu. Horo mai tsanani ba ya gyara tarbiyya ko kadan. Dukan yara kawai wata hanya ce ta bata rayuwarsu. Duka yana koyawa yara cewa, amfani da karfi da iyayensu suke yi shi ne hanya mafi inganci wajen warware rashin fahimta ko wani sabani tsakanin mutane.

Dukan yara shima yana aika sako mai rikitarwa ga yara cewa, koda yake ba zasu doki wasu yara ko manya da tsofaffi ba, amma ana nuna musu yana da kyau ga manya, waɗanda suka fi girma da ƙarfi, su doki yara, waɗanda galibi ƙanana ne kuma masu rauni. Yara suna koyon abubuwa ne daga abin da iyayensu suke yi, ba kawai daga abin da suke faɗi ba.

Kuma girmamawa ba daya take da tsoro ba. "Dabi’a mai kyau" da aka gina ta saboda tsoron azabtarwa na nufin cewa yaro yana nuna dabi’a mai kyau ne kawai saboda tsoron duka ko hukunci mai tsanani amma ba dan hali nagari ba. Amma idan iyaye suka nuna girmamawa da mutunta yara da wasu mutanen, da kare mutuncinsu na ɗan adam, yara zasu koyi tarbiyya. Idan iyaye suka yiwa yaransu tarbiyya, ta hanyoyi na mutunci ba tare da amfani da horo mai tsanani ba yaran zasu koyi darasin cewa, ana iya warware matsaloli cikin girmamawa, ba tare da anyi duka ko wani abu maras kyau ba.

Horon duka da sauran nau'in azabtarwa da na wulakantarwa ba zasu haifar da halaye masu kyau ba. Baya ga gyara halaye tarbiyyar yara ba tare da duka ba tana koyawa yara cewa a koda yaushe ya kamata su rika tunani akan abinda zasu aikata da kuma abinda zai kasance sakamakon abinda suka aikata. Yana kyau gwamnatoci su tallafawa iyaye wajen bada tarbiyya mai nagarta ga yara. Akwai bayanai akan haɓaka kyakkyawar halayyar yara da zasu amfani iyaye idan aka fassara su kuma aka sauya musu fasali domin a yi amfani dasu a kowacce kasa.



# Idan aka haramta horo mai tsanani, wannan ba zai sa a muzgunawa yara ba ta hanyoyin da zasu fi duka barazana ga tunaninsu da rayuwarsu?

Yara suna da bukatar samun hakkin kariya daga dukkan nau'in azabtarwa ga jikin mutum, har ma daga duk wasu nau'in azaba ko kaskanci ko cutarwa. Dole sai an danganta canza dokoki da kuma wayar da kai da sauya tunanin iyaye domin su fahimci yadd ake yin tarbiyya ba tare da amfani da duka ba.

Iyaya suna son yaransu su yi rayuwa mafificiya. Iyayen da suke dukan 'ya 'yansu ko suka zalunce su ta wasu hanyoyi – suna jin haushi da bacin rai daga baya. Yawancin iyaye za su yi maraba da shawara da tallafi akan yadda za a iya warware rikice-rikicen yaransu ba tare da amfani da kowane irin karfi ba, ta hanyar nuna tausayawa. Idan aka tashi daga duka da cin mutuncin yara zuwa basu daraja da kuma daukarsu a matsayin mutane, rayuwar iyalai zata inganta sosai ga kowa da kowa.

# Idan aka sa horo mai tsanani cikin manyan laifuka, ba za a daure iyaye da yawa ba kuma a karbe yaran a kai su reno?

Makasudin yin dokokin haramta horo mai tsanani ga yara ba wai ana so ne a jefa iyaye da dama a gidajen yari ba. Ana haramta hukunci mai tsanani ne domin kare hakkokin yara da kuma gina al'umma bisa hulda da yara cikin mutunci da kuma daraja. Koda a kasashen da doka ta haramta yiwa yara horo mai tsanani babu wata alamar cewa yin haka ya haddasa jefa iyayen yara dama cikin gidajen yari.

Haramta horo mai tsanani yana baiwa hukumomi damar sauke nauyin kare hakkin yara da ya rataya a wuyansu. Dalilin haramta horo mai tsanani ga yara shi ne ilimantarwa – aika sako zuwa cikin gidajen iyalai cewa, doka ta haramta yiwa yara horo mai tsanani. Yadda aka haramta dukan duk wani mutum haka ma an haramta dukan yara. Bayanai da zasu yi jagora ga wadanda suke karewa da kula da yara; kamar 'yan sanda da kuma hukumomi masu kare dokoki dole ne su maida hankali akan kare yara daga dukkan cin zarafi ko zalunci. Hukunci na doka da tsoma bakin hukuma ba zasu amfani yara ba, sai dai idan sune kadai hanyoyin da suka rage da za'a bi domin kare yara daga kowanne irin cutarwa.





A cikin Sharhinsa na 8, Kwamitin Kare Hakkin Yara yayi bayanin ka'idodi biyu da ya kamata su tabbatar da cewa haramcin horo mai tsanani ga yara bai haddasa hukunta iyaye da dama ba:

1. Ka'idar 'de minimis' – dake nufin cewa bai kamata dokar tana shiga kananan maganganu ba, wanda dan haka ne ma karamin sabani tsakanin manya ba ya kaiwa ga zuwa kotu. Haka ya kamata lamarin ya kasance dangane da hukunci da ba shi da tsanani ga yara.

2. Saboda dogaron yara da kuma kusancinsu da iyayensu, kamata yayi a yi taka tsantsan wajen hukunta iyaye bisa laifin yin horo mai tsanani ga yara. Za'a yi hukuncin ne kawai idan ya zama dole domin kare yara daga cutarwa.

# Ba daidai ba ne iyaye su dan doki yara don hana su cutar da kansu?

Dukan yara don hana su cutar da kansu ba shi da wata ma'ana! Shin zaku iya tunanin ba da shawara ga iyaye cewa idan yaransu suna cikin haɗari ya kamata a doke su? Tabbas ba za'a yi haka ba.

Dole iyaye su yi amfani da sassan jikinsu a zahiri don kare yara – musamman jarirai da yara kanana – a koyaushe. Hanya ce ta reno daga Allah. Idan yaro ya yi rarrafe zuwa wurin wuta, ko kuma yana tafiya akan titi mai haɗari, a zahiri iyaye suna amfani da karfin jikinsu don hana su – ta hanyar kama su, ɗaukarsu, da gaya musu haɗarin da suka fuskanta. Amma ji musu ciwo ta hanyar yi musu duka gaba ɗaya ya sabawa kokarin nuna musu cewa dole ne su koyi kiyaye kansu daga hatsari kowanne iri ne. Kuma kafin su girma su san hatsarin komai da komai iyaye ne zasu ci gaba da kare su. Kamar yadda Kwamitin Kare Hakkin Yara yayi bayani:[12]

"...Renon yara da kulawa da su, musamman jarirai da yara kanana, na bukatar daukar matakan sa ido sosai da daukar mataki na zahiri domin kare su daga duk wani hadari. Wannan ya banbanta sosai da amfani da horo mai tsanani, azabtarwa ko nuna karfi dake sa yara cikin kaskanci da wulakanci. A matsayinmu na manya, mun san bambanci tsakanin bada kariya ta zahiri da azabtarwa; iya rarrabe wannan ba abu ne mai wahala ba musamman ma a batun da ya shafi yara."

12. Bayani kai tsaye, No. 8 Sakin layi. 14.

Akwai banbanci a fili tsakanin amfani da karfi wajen kare yara daga dukkan cutarwa, da kuma amfani da karfi da gangan da nufin cutar da yara da sunan tarbiyya. A kowacce kasa, a zahiri da badini, doka ta amince da a yi amfani da karfi domin kare mutane daga kowacce irin cutarwa. Amma haramta amfani da horo mai tsanani wajen tarbiyyar yara ba zai shafi tanadin doka na amfani da karfi wajen kare rayuwar mutane ba.



# Hada kan Kasashe ta yanar gizo:

**www.endcorporalpunishment.org**

Ana iya samun cikakken bayanai a shafin internet na (Global Initiative) game da duk abubuwan da suka shafi haramta horo mai tsanani ga yara, kamar:

- Cikakkun rahotanni da bayanai akan yadda lamarin yake a kowacce kasa.
- Jadawali na duniya akan halaccin horo mai tsanani ga yara da kuma damar da ake da ita ta yin sauye-sauye ga dokoki.
- Yadda MDD da hukumomin kare hakkin bil'adama na nahiyoyin duniya suke warware matsalar horo mai tsanani ga yara, da kuma jagora akan yadda za'a yada wadannan sauye-sauye.
- Akwai takaitattun bayanai akan sakamakon bincike akan matsalar horo mai tsanani ga yara da kuma tasirinsa akan rayuwar yara, da manya da kuma al'umma baki daya.
- Akwai bayani don tallafawa wajen aiwatar da haramcin.
- Akwai bayanai masu yawa daga kasashe da sassan duniya da kuma bayanai cikin harsuna daban-daban.



# Lokaci yayi na kawo karshen horo mai tsanani ga yara. Yara suna da 'yancin girmamawa da kariya daidai wa daida daga kowanne nau'in tashin hankali a yanzu!

**Gamayyar Kasashe don kawo Karshen Horo mai Tsanani ga Yara**

Gamayyar kan Kasashe don kawo Karshen Horo mai Tsanani ga Yara na ci gaba da kira ga kasashen duniya su haramta duk wani nau'i na horo mai tsanani ga yara kuma muna bada bayanai da tallafin fahimta wajen kawo sauye-sauye ga dokoki don kare yara a duk duniya.

*www.endcorporalpunishment.org*

*info@endcorporalpunishment.org*

*www.twitter.com/Glendcorpun*

*www.facebook.com/Glendcorporalpunishment*

**Save the Children ta Sweden**

Save the Children Sweden tana kiran a soke duk wani horo mai tsanani ga yara, a kowanne hali da kuma yanayi. A cikin 1979 Save the Children Sweden ta ba da gudummawa ga Sweden ta zama kasa ta farko a duniya da ta haramta hukunci mai tsanani ga yara. Kungiyar tana aiki don jawo hankali akan batun da kuma tabbatar da cewa an sanya wannan batu a jerin batutuwan da za'a rika tattaunawa a fagen siyasa a duniya.

*info@rb.se*

*www.raddabarnen.se*

*resourcecentre.savethechildren.net*

GLOBAL INITIATIVE TO
End All Corporal
Punishment of Children

Save the Children